BAYANI GA DALIBAI MASU SHA'AWAR KARATU A JAMI'AR KIMIYAR LAFIYA DAKE TEHRAN – IRAN
( TEHRAN UNIVERSITY OF MEDICAL SCIENCES – TUMS IRAN )
CIKIN HARSHEN HAUSA


Tehran University of Medical Sciences
Office of Vice-Chancellor for Global Strategies and International Affairs
Directorate of International Development


Language: Hausa

## BAYANI GA DALIBAI MASU SHA'AWAR KARATU A JAMI'AR KIMIYAR LAFIYA DAKE TEHRAN – IRAN (TEHRAN UNIVERSITY OF MEDICAL SCIENCES – TUMS IRAN) CIKIN HARSHEN HAUSA

Ita dai wannan makaranta (TUMS) tana cikin birnin Tehran a kasar Iran. Kasar Iran tana daya daga cikin kasashen Gabas ta tsakiya. Kuma tana da yaawan jama'a har kimanin miliyan sabain da biyar (75 miliyan) tare da fadin murabba'in kasa har 1,648,195 sq Km.

Tehran shine babban birnin kasar. Kuma yana dauke da mutane miliyan takwas (8 miliyan). Sannan kuma shine birni na sha tara (19) a yawan jama'a a duniya.

Mutanen kasar Iran suna maganane da harshen Farisanci wanda shine yaren kasar.

Wannan Jami'ar (TUMS) tana bawa dalibai 'yan kasashen waje wajen kwana kyauta wanda aka kawatashi da Gado da Kujerun Kushin da kayan dakin girki da abin dumama abinci (microwave oven) da Firiji da injin wanki (washing machine) da Talabijin da kuma yanar gizo-gizo duk kyauta.

Akwai dammar samun aikinyi acikin makarantar ga dalibin/dalibar daya/ta cancanta a duk bayan zangon karatu na farko (first semester).

A TUMS zangon karatu na 'Fall' yana farawane a watan Satumba da kuma na lokacin karatu na Spring da yake farawa a watan Janairu na kowacce shekara. Zangon karatun gaba daya yana kasancewa wata Tara (Wata - 9) san nan kuma dalibai na kasancewa cikin hutu alokacin Summer.

## ABUBUWAN DA AKE BUKATA DON SAMUN GURBIN KARATU A WANNAN JAMI'A

*MASU NEMAN DIGIRI NA FARKO

Mai neman digiri na farko shine wanda ya gama Sakandire ko Difiloma yake son ya sami B.Sc. ko M.D. ko D.D.S. ko kuma Pharm.D. Idan ana bukatar samun Karin bayani sai a duba adireshin yanar gizo-gizo na makarantar kuma anan za'a sami Fom din acike. Lokacin cike Fom din za'a turo da takardun shaidar kamala makaranta.

Wadan nan abubuwa sune ake bukata:

1. Takardar da zata bayyana dalilin da yasa ake da sha'war yin karatu a Jami'ar da kuma bangaren da ake son a kware ko samun horo da kuma matakin karatu.
2. Takardar tarihin rayuwa (Resume ko CV).
3. Takardar Difiloma wacce ta kunshi darasin Biology da Chemistry da Physics da Mathematics da Physiology. Takardar shedar kamala Sakandire kunshe da darasin Biology da Chemistry da Physics da Mathematics da English. Duk biyun ko ta sakandire kadai in ba Difilomar.
4. Shedar kwarewa a Turanci. Wato kamar su jarabawar TOEFL ko ILETS (kafin mutum yagama ana son ya sami maki wanda bai gaza 5.5 ko makamancin haka.
5. Takardun bayani akan dalibi / ba wanda akeson wasu malamanka / ki ko wanda yasanka / ki zasu rubuta (Referee/ Recommendation letters) mutum biyu.
6. Hoton Fasfo guda daya.
7. Shafuka masu mahimmanci na Fasfon na Tafiya wata kasa. Shafin da hotonka / ki da kuma bayaninka / ki yake a Fasfo din.

MASU NEMAN BABBAN DIGIRI

Wa dannan sune daliban da suka riga sukayi digirin farko zasu yi na biyu ko kuma na uku. Don Karin bayani sai a shiga shafin yanar gizo-gizo na wannan makarantar.

Mai son yin babban digiri shima zai cike Fom din a shafin yanar gizo-gizo- tare da turo wadannan takardun:

1. Takarda da zata bayyana dalilin da yasa ake da sha'war yin karatu a Jami'ar da kuma bangaren da ake son a kware ko samun horo da kuma matakin karatu.
2. Takardar tarihin rayuwa (Resume ko CV).
3. Takardar shedar kammala karatun digiri na daya da na biyu ga mai son yin digiri na uku (B.Sc. da M.Sc. ko M. Phil). Ga wanda yake son yayi digiri na biyu kuwa zai bukaci takardar digiri na daya da kuma ta Difiloma ko Sakandire dinsu (ko maka mancin haka kamar takardar shedar kammala M.B.B.S. da sauransu) ko wacce tare da Taransikirif dinta (da jimlar maki kamar ¾ ko makamancin haka).
4. Shedar kwarewa a Turanci. Wato kamar su jarabawar TOEFL ko ILETS (kafin mutum ya gama ana son ya sami maki wanda bai gaza 5.5 ko makamancin haka.
5. Takardun bayani akan dalibi / ba wanda akeson wasu malamanka / ki ko wanda yasanka / ki zasu rubuta (Referee/ Recommendation letters) mutum uku.
6. Hoton Fasfo guda daya.
7. Shafuka masu mahimmanci na Fasfon na Tafiya wata kasa. Shafin da hotonka / ki da kuma bayaninka / ki yake a Fasfo din.

## HANYAR TUNTUBARSU


∆ Takwatin Gidan Waya

Tehran University of Medical Sciences (TUMS)
Office of Vice-Chancellor for Global Strategies and International Affairs
Directorate of International Affairs and Development
Marketing and Recruitment Division
Number 21, Damesgh St.
Vali-e Asr Ave., Tehran 14155-5799 Iran.

∆ Ta Hanyar Yanar Gizo (E-mail)

Adimishin: admission_ic@tums.ac.ir
Marketing: oia-ic@sina.tums.ac.ir

∆ Ta Hanyar Nambar Waya

Nambar Talafon
Adimishin: (+9821) 88896696
(+9821) 88898531

Nambar Fax
(+9821) 88852655

Shafi Yanar Gizo-Gizon Jami'ar Shine: www.gsia.tums.ac.ir

www.gsia.tums.ac.ir